## SŨRATUL FAJR سُورَةُ الفَجۡرِ

Tana karantar da cẽwa girmamawa da ĩmãni da taƙawa take, bã da sãmun dũkiya ko kyãwon halitta ko mulki ba.

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Inã rantsuwa da alfijiri,

وَٱلۡفَجۡرِ ١

*2.* Da darũruwa gõma.

وَلَيَالٍ عَشۡرٖ ٢

*3.* Da (adadi na) cikã da (na) mãrã.

وَٱلشَّفۡعِ وَٱلۡوَتۡرِ ٣

*4.* Da dare idan yana shũɗewa,

وَٱلَّيۡلِ إِذَا يَسۡرِ ٤

*5.* Ko a cikin waɗannan akwai abin rantsuwa ga mai hankali (da yake kange shi daga zunubi)?

هَلۡ فِي ذَٰلِكَ قَسَمٞ لِّذِي حِجۡرٍ ٥

*6.* Ba ka ga yadda Ubangijinka Ya aikata da Ãdãwa ba?

أَلَمۡ تَرَ كَيۡفَ فَعَلَ رَبُّكَ بِعَادٍ ٦

*7.* Iramawa mãsu sakon[1] ƙĩrar jiki.

إِرَمَ ذَاتِ ٱلۡعِمَادِ ٧

*8.* Waɗanda ba a halitta kwatankwacinsu ba, a cikin garũruwa (na dũniya).

ٱلَّتِي لَمۡ يُخۡلَقۡ مِثۡلُهَا فِي ٱلۡبِلَٰدِ ٨

*9.* Da Samũdãwa waɗanda suka fasa duwãtsu a cikin wãdi[2] (suka yi gidãje)?

وَثَمُودَ ٱلَّذِينَ جَابُواْ ٱلصَّخۡرَ بِٱلۡوَادِ ٩

---

(1) Tsawo mai ma'ana.

(2) Wãdil ƙura, sunan wuri ne kusa da Madina wajen Syria, wato Sham.

*10.* Da Fir'auna mai turãku,

*11.* Waɗanda suka ƙẽtare iyã-karsu, a cikin garũruwa?

*12.* Sabõda haka, suka yawaita yin ɓarna a cikinsu.

*13.* Sabõda haka Ubangijinka Ya zuba musu bũlãlar azãba.

*14.* Lalle ne Ubangijinka Yana nan a mafaka.

*15.* To, amma fa mutum idan Ubangijinsa Ya jarraba shi, wãto Ya girmama shi kuma Ya yi masa ni'ima, sai ya ce, "Ubangijina Yã girmama ni."

*16.* Kuma idan Ya jarraba shi, wãto Ya ƙuntata masa abincinsa, sai ya ce "Ubangijina Ya walãkanta ni."

*17.* A'aha! Bari wannan, ai bã ku girmama marãya!

*18.* Bã ku kwaɗaitã wa jũnanku ga (tattalin) abincin matalauci!

*19.* Kuma kuna cin dũkiyar gãdo, ci na tãrãwa,

*20.* Kuma kuna son dũkiya, so mai yawa,

*21.* A'aha! Idan aka niƙa ƙasa niƙewa sosai,

*22.* Kuma Ubangijinka Ya zo, alhãli malã'iku na jẽre, safũ-safu,

*23.* Kuma a ranar nan aka zo da Jahannama. A ranar nan mutum zai yi tunãni. To, inã fa tunãni yake a gare shi!

*24.* Yana dinga cẽwa, "Kaitona, dã na gabatar (da aikin ƙwarai) domin rãyuwata!"

وَفِرْعَوْنَ ذِي الْأَوْتَادِ ١٠

الَّذِينَ طَغَوْا فِي الْبِلَادِ ١١

فَأَكْثَرُوا فِيهَا الْفَسَادَ ١٢

فَصَبَّ عَلَيْهِمْ رَبُّكَ سَوْطَ عَذَابٍ ١٣

إِنَّ رَبَّكَ لَبِالْمِرْصَادِ ١٤

فَأَمَّا الْإِنسَانُ إِذَا مَا ابْتَلَاهُ رَبُّهُ فَأَكْرَمَهُ
وَنَعَّمَهُ فَيَقُولُ رَبِّي أَكْرَمَنِ ١٥

وَأَمَّا إِذَا مَا ابْتَلَاهُ فَقَدَرَ عَلَيْهِ رِزْقَهُ فَيَقُولُ رَبِّي
أَهَانَنِ ١٦

كَلَّا بَل لَّا تُكْرِمُونَ الْيَتِيمَ ١٧

وَلَا تَحَاضُّونَ عَلَىٰ طَعَامِ الْمِسْكِينِ ١٨

وَتَأْكُلُونَ التُّرَاثَ أَكْلًا لَّمًّا ١٩

وَتُحِبُّونَ الْمَالَ حُبًّا جَمًّا ٢٠

كَلَّا إِذَا دُكَّتِ الْأَرْضُ دَكًّا دَكًّا ٢١

وَجَاءَ رَبُّكَ وَالْمَلَكُ صَفًّا صَفًّا ٢٢

وَجِيءَ يَوْمَئِذٍ بِجَهَنَّمَ يَوْمَئِذٍ يَتَذَكَّرُ
الْإِنسَانُ وَأَنَّىٰ لَهُ الذِّكْرَىٰ ٢٣

يَقُولُ يَا لَيْتَنِي قَدَّمْتُ لِحَيَاتِي ٢٤

*25.* To, a rãnar nan bãbu wani mai yin azãba irin azãbar Allah.

فَيَوْمَئِذٍ لَّا يُعَذِّبُ عَذَابَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿٢٥﴾

*26.* Kuma bãbu wani mai ɗauri irin ɗaurinSa.

وَلَا يُوثِقُ وَثَاقَهُۥٓ أَحَدٌ ﴿٢٦﴾

*27.* Yã kai rai mai natsuwa!

يَٰٓأَيَّتُهَا ٱلنَّفْسُ ٱلْمُطْمَئِنَّةُ ﴿٢٧﴾

*28.* Ka koma zuwa ga Ubangijinka, alhãli kana mai yarda (da abin da Ya ƙaddara maka a dũniya) abar yardarwa (da sakamakon da zã a ba ka a Lãhira).

ٱرْجِعِىٓ إِلَىٰ رَبِّكِ رَاضِيَةً مَّرْضِيَّةً ﴿٢٨﴾

*29.* Sabõda haka, ka shiga cikin bãyiNa (mãsu bin umurni a dũniya).

فَٱدْخُلِى فِى عِبَٰدِى ﴿٢٩﴾

*30.* Kuma ka shiga AljannaTa (a Lãhira).

وَٱدْخُلِى جَنَّتِى ﴿٣٠﴾

## SŨRATUL BALAD سُورَةُ البَلَدِ

Tana karantar da cewa mutum an halitta shi cikin wahala, ko mai amfanin sa idan ya bi umurnin Allah ko kuwa mai cũtar sa idan ya saɓa wa umurnin Allah.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

*Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai.*

*1.* Bã sai Na yi rantsuwa da wannan gari[(1)] ba.

لَآ أُقْسِمُ بِهَٰذَا ٱلْبَلَدِ ﴿١﴾

(1) Allah Ya ce bã sai Ya yi rantsuwa da Makka ba sa'an nan zã a san darajarta, a lõkacin da Annabi yake a cikinta, kuma shi yana da haƙƙin zama a cikinta mahaifansa da zurriyarsa duka, ko da yake zai yi hijira sabõda fitinar kãfirai mãsu halaka dũkiyarsu kan adãwa da shi. Dã sun yi amfãni da dukiyar ga ayyukan alhẽri, dã yã fi musu.